BU African Studies Center LANGUAGE PROGRAM, 232 BAY STATE ROAD, BOSTON, MA 02215
www.bu.edu/Africa/alp
africa@bu.edu
617.353.3673

# Skit 2: A bar kaza cikin gashinta

| | |
|---|---|
| **Yazi Dogo:** | **Wannan ma'ana shi ne, idan kana son mutum, kar ka shiga cikin tambaye-tambayen halinshi).** |
| Mai Gari (MG): | Shi hwa Yahaya. Abin da ya sa ni ce mu tantamna, karatu in ba sadaka hwa hauka yake sawa. Shi yanzu wannan da yake son a je a ɗauke shi **dibite**, bara hwa kun ga yadda ya yi. |
| A1: | Salamau alaikum. |
| MG: | Ba aikin da ya yi mumu. |
| MG and others: | Amin alaikas salam. |
| A1: | Ranka ya daɗe Mai gari. Kuna lahiya? |
| MG: | Lahiya lau. Lahiya lau. |
| A1: | **Kauna** nan tawa ce na kawo. |
| MG and others: | To. |
| A1: | Saboda ƙarar mutanen garin nan naka. |
| MG and others: | To.... |
| MG: | Ina take ƙaunar taka? |
| A1: | Suwaiba! Ya ki! Taho! |
| MG: | Zamna can baya. Zamna can. Koma can baya. |
| A1: | Zamna can baya! Koma can baya ki zamna. To zamna nan ... Yanzu ka duba ka gani Mai gari, saboda Allah saboda Annabi, mutanen garin nan mutanen kirki ne? Duba ka gani **wata kama** gareta. |
| MG: | Uhmmm! |

© Boston University

| | |
|---|---|
| A1: | Dan Allah a **hidda** mata **haki**nta. Ka duba ka gani sun mata **ciki** mutanen garin nan. A nan akwai gaskiya? |
| MG: | Ummm. ... A hudda mata hakinta. |
| A1: | Ka duba ka gani hwa! |
| MG: | Ummm. |
| A2: | A'a. Mai gari. A bar kaza cikin gashinta. Saboda hwa in aka **hige**ta in ba a ga ta **zama** ƙarama ba, a ga ba ta da kyau. |
| MG: | Yau! Wai ca ya yi .... |
| A3: | A'a. Aikin ga ko kai ka yi shi dai? |
| A2: | A'a. Haram! In haka ne, shegiya kaza, a hige ta. |
| MG: | Um, um. |
| A2: | A hige kaza! Mai Gari, .... |
| MG: | A'a. Shi hakinta ne yake so. |
| A2: | I, a huddo shi! |
| MG: | A'a ... |
| A2: | A huddo hakinta. |
| MG: | To, kai yanzu ya ka gani? |
| A2: | E, a huddo hakinta! |
| A3: | To yanzu tunda ***haka ta kasance***, kai **bawan Allah** a tambaye ta wane ne? |
| MG: | Mm, mm! Kamar yadda ya faɗi, a bar kazar cikin gashinta. In **Allah ya sabke ta lahiya**, ko ba haka ba ... |

| | |
|---|---|
| A4: | Allah ya ba ka nasara, haki ya ce ... a hidda hakin ... |
| A3: | A'a. Mai gari. Haki ya ce, a hidda mai haki ko? Yanzu kai ka tambaye ta wane ne? |
| A4, A2: | E! E! |
| A2: | A hidda hakinshi, a hidda hakinshi. Amma kai Kalla ka ce ni ne! |
| MG: | Wai kamar yadda ya ce Allah ya sauke ta lahiya ... |
| A2: | Suwaiba! Bari **wasar ƙasa** Suwaiba. Nan wurin mai gari ne. Bari wasar ƙasa! Tsaya manan! |
| A4: | Sai a jira hal, za.. hal lokacin ko? |
| A3: | A'a. Ba zancen a jira. Mai gari, kai ta... **tambaye ta**! |
| A4: | Ko da yake ba a tambayar mahaukaciya ... |
| All: | Tambaye ta! Tambaye ta! E! Tambaye ta! |
| A2: | **Ranka ya daɗe** Mai gari. E. Suwaiba! I magana, Suwaiba! I magana! |
| A4: | Ba ta magana, haba! |
| A2: | Su wane ne suka yi miki wannan abin? |
| A3: | Yauwa! |
| A3: | Wane ne ya yi miki wannan abun? |
| A4: | **Ba ta da baki**! |
| Suwaiba: | Ina ni sani ni. Tun da **wanga** ya yi, wanga ya yi. **Hadda** su Mai gari ma! |
| MG: | To ba ga irinta ba! |

| | |
|---|---|
| Others: | **Subahanallahi!** Subahanallahi! |
| MG: | **Ba ga irinta ba**? Ba ga irinta ba? Na ce muku a bar kaza cikin gashinta, ga shi.... |
| A3: | Yanzu Mai gari, kai da kanka? Kai da kanka? **Wakili**n mutane a garin nan? Ka **aikata** wannan ɗanyen aiki? |
| MG: | Diba! Ba haka ba ne. Ba haka ba ne. An ce a bar kaza cikin gashinta, an bar ta. Kun zo kun **tona** ma mutane **asiri!** |
| A3: | Kazar wace ce? |
| MG: | Ku tashi na **ɗage shari'a** to! Na ɗage shara'ar na ce, a tashi! |
| A3: | Ina hwa ka ɗage shara'a Mai gari? |
| MG: | Na ɗage! Na ɗage shara'a! |
| A3: | Kai yanzu Mai gari kai wakilin mutane? Mm? |
| MG: | Ke tashi je ki! Allah sauke ki lahiya! |